Ukkaz da Mijna da Thul-Majaz a lokacin Jahil;iyya Kasuwanni ne sai kuke ganin laifi ne kuyi kasuwanci a cikinsu lokacin aikin Hajji, Sai Allah ya saukar da: Babu laifi akan ku ku nemi Falala daga Ubangijinku" Bakara:198 a cikin lokacin Hajji

An rawaito daga Abdullahi Bn Abbas -Allah ya yarda da su- ya ce: "Ukkaz da Mijna da Thul-Majaz a lokacin Jahil;iyya Kasuwanni ne sai kuke ganin laifi ne kuyi kasuwanci a cikinsu lokacin aikin Hajji, Sai Allah ya saukar da: Babu laifi akan ku ku nemi Falala daga Ubangijinku" Bakara:198 a cikin lokacin Hajji"
[Ingantacce ne] [Buhari ne ya rawaito shi]

Wadan nan wurare sun kasancr kasuwanni ne ga Mushirikai kafin zuwan Musulunci suna yin kasuwanci a cikinta a lokutan Hajji, sai Sahabbai –Allah ya yarda das u- suka ji tsoron yin zunubi in sunyi kasuwanci a cikinta a lokacin aikin hajji, sai allah ya saukar da wannan Ayar don tayi musu bayanin Kasuwanci a cikin lokacin Aikin Hajji bat a bata aikin Hajji ta hanayar Shari’a, kan cewa Kasuwanci cikin Hajji halas ne, sai dai abun day a fi kuma yafi dacewa shi ne Mutum ya yi aikin Hajji ba tare da hada da komai ba, to wannan shi ne mafifici

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/2755